**EPISODE 17**

Characters

*Tina*

*Hannah*

*Laraba*

*Dr. Daoud*

*Danjuma*

*Kande*

SCENE 1

**Danjuma's House, morning**

1. **MUSIC:** **THEME MUSIC**

2. **SFX:** **SOUNDS OF RUSHING WATER INTO A BUCKET**

3. **TINA:** **(SINGING ROMANTIC MUSIC)** *Danjuma don make me fall in love, he don make me fall in love…*

4. **HANNAH: (CALLING OUT)** Tina! Tina!!

5. **TINA:** **(SINGING)** *He don make me fall in love, make me fall in love…*

6. **HANNAH**: Tiiinnnnnaaaaaa!

7. **TINA: (MUTERING TO HERSELF)** Ohhh! Me wannan Hannah Take so kuma? (ALOUD, CALLIN GOUT TO HANNAH) Naam?
Yaruwata Hannah, Ina waje.

8. **SFX:** <u>SOUND OF SLOW FOOTSTEPS COMING ON MIC</u>

9**. HANNAH**: Ah Tina, Ina kwana. Babu aiki ne yau?

10. **TINA:** Ah yar uwata Hannah, na dai ce bari in wanke wasu kaya ne kafin in shirya.

11. **HANNAH**: toh Inason ki taimaka ki saya mun katin waya akan titi.

12. **TINA:** Babu damuwa , Yar u wata. Bari in gama shanya wannan kayan.

13.**HANNAH:** Bari in tamaka miki. Ke da Danjuma dai Kun sani na zama malalaciya. **(PAUSE)** Ah Tina, Kin san ba sai kin wanke mun kaya na ba. Nima zan iya wankewa da kaina. Ban yi tsammanin za ki wanke ba.

14. **TINA:** Ba Matsala bace a gareni Yaruwata Hannah………

15. **HANNAH: (INTERRUPTS, GASPS)** Tina!

16. **TINA:** Mene? Menene wannan?

17. **HANNAH: (ANGRILY)** Tina? Wannan ba kayan mijina ne ba? Ehn Tina?!

18. **TINA: (DEFENSIVELY)** Ehn, lokacin da naje kwaso kayanki ne, sai naga kwandon shi ya cika.

19. **HANNAH: (ANGRILY)** Tina, Kina neman ki wuce iyakarki a nan, kalli harda ma kamfensa … saboda me haka? ba hurumin ki bane.

20. **TINA:** **(ANGIRLY)** Dakata, duk wannan matsalar saboda na taimaka na wanke kayan da kika kasa wanke wa Hannah?

21. **HANNAH: (FURIOUS)** Ehn Tina, me kikace?

22. **TINA:** Hannah, ko karyane? kalla a kwai wankin mako daya da kika ki wankewa acikin kwandon Danjuma.

Abin da nake cewa shine, idan ina da miji kamar Danjuma, bazantaba barin kwadon wankin sa ya cika ba.

23. **HANNAH:** Ehehn Tina! So Shirinki dama ke nan ! Kina son a dauke ni matar banza. Kina yi wa mijina girki ba tare da sanina ba. Idan kuma ya aiko ki da sako ba ki gayamun. Har rannan na kama ki kina kara dawadawa a cikin miya ta.

24. **TINA:** **(INCREDULOUSLY)** O-ho wato kin kullaceni a zuciyarki, eh, Hannah! Saboda abune mara kyau taimaka miki Kaddamar da ayyukan da ya kamata ki yi a halin da ki ke ciki?

25. **HANNAH: (ANGRILY)** Tina kin san abin da kike yi! A wane Kasace aka yarda ki wanke wa mijina kamfensal wannan ya zama kashedi a gareki, ki bar mun mijina ki nemi naki.

26. **TINA:** Kalli, idan kina da tantama kan zamantakewar ku da mijinki Hannah, don Allah kada ki daura mun laifi.

27. **MUSIC:** <u>BRIDGE MUSIC</u>

SCENE 2

OUTSIDE INNA's COMPOUND

28. **SFX:** <u>**SOUNDS OF A CAR ENGINE BEING TURNED OFF.**</u>

29. **DAOUD:** Mun Kawo, Laraba

30. **LARABA:** Na gode Daoud da ka rage mun hanya.

31. **DAOUD: (INTERRUPTS)** Na gode Laraba da kika bani daman yin haka. **(TEASING)** Ko da yake daga karshe kamar ni nake rokon ki da ki bani daman in kai ki gida.

32. **LARABA: (LAUGHS**) Ehn bana son in takura maka ne, saboda na san ba bangare daya muke ba.

33. **DAOUD:** Babu damuwa, Laraba. Wannan Karamin abu ne. Idan da hali, da nayi fiye da haka domin in nuna miki zurfin so da kaunar da nake yi miki.

34. **LARABA: (LAUGHS)** Ah Daoud, Kana sa Kaina yana kara Kumbura.

35. **DAOUD:** Laraba, gaskiya na fadi na kagara mu sadu da Kawunki domin in sanar dashi kaunar da na ke yi miki. Kai!

36. **LARABA: (LAUGHS)** Haba Likita duk zaka gaya wa Kawuna wannan.

37. **DAOUD:** Kwarai, Kin riga kin bani lambar wayar sa da kuma addreshin sa : kin ga sai in cigaba kawai.

38. **LARABA:** (LAUGHS) Haba likita Daoud, ban san kai mai zafin nama bane haka.

39. **DAOUD:** Da gaske, laraba na yi murna kwarai da jin soyayya. Bayan rasuwar matata na fitar da rai daga soyayya a rayuwa.

40. **LARABA:** Baka taba bani labarin abin da ya faru da ita ba, Daoud.

41. **DAOUD:** Wallahi ta rasu a cikin hatsarin mota.

42. **LARABA**: (EXCLAIMS) Oh Allah!

43. **DAOUD:** Laraba, wannan babban abin alajabine a rayuwata.

44 **LARABA:** Kai! Allah ya jikanta.

45 **DAOUD:** Ya jikansu.

46. **LARABA:** Ban gane ba, Daoud

47. **DAOUD:** Dukansu suka rasu ranar, yaro na da matata.

48. **LARABA:** Wayyo Allah na!

49 **DAOUD: (SIGHS)** Ta samu matsala a wurin haihuwa, sai muka bada shawara ayi mata aiki kafin ranar haihuwar.

50. **LARABA: (INTERRUPTS**) Kayi hakuri da na tunasar da kai abin da ya wuce.

51. **DAOUD: (SIGHS)** Babu damuwa, Sunanta Maryam, ga kirki da kauna **(EXHALES LOUDLY)** Lokacin haihuwar ta bai yi ba saboda haka sai da suka zauna a asibitin har mako hudu.

52**. LARABA:** Ayah

53. **DAOUD:** An Sallame su daga asibitin, amma tafi son zama kusa da jarriyar **(SIGHS)**

54. **LARABA:** Ayah

55. **DAOUD:** Ina cike da Farin ciki da aka ce zamu iya tafiya gida da yaron. A kofar asibitin na waywaya inga inda yaro na yake, kafin in juya sai wata

babbar mota da birki ya kwace mata ta daki motar mu duk suka rasu anan take.

56. **LARABA: (INTERRUPTS)** Wayooo! Kai ke tuki kenan a lokacin da suka rasu!

57. **DAOUD: (TAKEN A BACK)** Hakane, amma hatsarine. (PAUSES)
Laraba, Fuskarki. Don Allah kada ki dauki alamarin da zafi. Na ga Kina girgiza.

58. **LARABA:** Wannan musun gamon katari yayi yawa ga mutum guda.

59**. DAOUD: (CONFUSED)** Mene? Haka ne amma hatsari na Faruwa. Kuma haka Allah ya so…..

60**. LARABA: (CUTS IN)** Kalli Likita, ya kamata in tafi, sai da Safe.

61**. SFX: <u>SOUND OF ONE CAR DOOR OPENING AND SLAMMING SHUT. FOLLOWED BY SOUND OF ANOTHER CAR DOOR OPENING AND SLAMMING SHUT</u>**.

62**. DAOUD: (CALLING OUT)** Laraba! Laraba? Me ya Farune? Menene matsalar? Dawo mana?

63. **MUSIC: <u>BRIDGE MUSIC</u>**

**<u>SCENE 3</u>**

DANJUMA’S OFFICE

64. **SFX: <u>SOUND OF KNOCK ON A WOODEN DOOR</u>**.

65 **DANJUMA:** Yes, Shigo Mana.

66. **TINA**: **(COMING ON MIC)** Ina Kwana, Yaya Danjuma.

67. **DANJUMA:** Ah Tina, Ina Kwana. Mallam Aliyu ya aike ki da filoline! Yayi kyau, Ki ajiye su akan tebur.

68**. TINA:** Yaya Danjuma, Mallam Aliyu yace abokan cinikin sun mayar da taron zuwa karfe hudu (4.00pm).

69. **DANJUMA: (MUTTERS TO SELF)** ya kamata in kira Hannah in gaya mata ba zan dawo da wuri ba. (TO TINA) yaya kike Tina? Yaya aikin yake?

70. **TINA: (SIGHS, DEPRESSED)** Lafiya lau, yaya Danjuma.

71. **DANJUMA**: Babu alamar haka a gareki, me ya Faru?

72 **TINA:** Babu Komai.

73 **DANJUMA:** Na tabbata wani abu ya Faru, gaya mun, Tina ko aikin ne da wahala?

74. **TINA:** (**SIGHS)** Babu, aikin ba wahala (**HESITANTLY**) amma dai, Danjuma, bana son in jawo maka matsalane a gida.

75. **DANJUMA: (CONFUSED)** A gida ? Kina da matsala a gida? Da wa? Hannah?

76. **TINA (SNIFFLING**) Haka ne **(WAILING)** Danjuma, ta tsane ni.

77. **DANJUMA**: Ah Tina, kada ki yi kuka mana na tabbata rashin fahimta ne. Hannah bata tsanan kowa. Gaya mun me yafaru.

78. **TINA: (SOBBING**) Ban san abin da nayi wa Hannah ba da take da zafi a kai na.

79. **DANJUMA**: Hannah? Ban yarda ba.

80. **TINA:** Da safen nan, Ina wanke kayan ka, Saboda in hana ta wanki ganin halin da take ciki, kawai sai ta fusata.

81. **DANJUMA: (SURPRISED)** Kan kayan wanki?

82. **TINA:** Bashi kadai ba tayi guna gunin cewa wani lokaci ina dafa maka abinci kuma muna cin abinci tare a tebur guda.

83. **DANJUMA:** Haba ai wannan so daya ya faru, a lokacin da ta tafi makaranta domin shawo kan matsalar takardar jarabawar ta.

84. **TINA: (SNIFFLING)**: Hm Danjuma  Duk wani abu da na yi, laifi ne a gareta. Ta kan yi guna gunin cewa na cika iya wa.

85 **DANJUMA:** Ban taba hirar ba. Kuma kwazo a aiki sai ya zama iya yi?

86. **TINA:** Ina kokarin rage mata aiki ne saboda na ga tana da ciki. Bana tunanin cutarwa.

87. **DANJUMA:** Na sani.

88. **TINA: (SIGHS)** Abin da yafi bata mun rai shine da tace mun wai in je in nemi nawa mijin (SOBBING)

89. **DANJUMA:** Ina zan shawo kan matsalar.

90. **TINA: (SOBBING)** Ba zan iya jure wa ba, Danjuma.

91. **DANJUMA:** Kada ki damu, na tabbata wannan rashin Fahimta ne kawai. Zan yi Magana da Hannah

SCENE 4

KANDE'S HOUSE

92. **SFX:** <u>**DOOR OPENING AND CLOSING**</u>

93. **KANDE:** Hannah!

94: **HANNAH:** Mama, kin dawo?

95. **KANDE:** Na dawo, kuma kamar hullum, kalle ki kina jirana a parlor. Me mijinki zai ce idan ya dawo gida kuma ba kya nan.

96. **HANNAH: (LAUGHS)** Suna da taro ne a offis kuma zasu dade , shiyasa nayi amfani da wannan dammar in zo in ganki.

97. **KANDE:** Yaya kike? Ina Fatan baya baki wahala?

98. **HANNAH:** Ina lafiya, Jaririn na lafiya wannan makon.

99. **KANDE (LAUGHS)** Daukarshi guda daya a lokaci guda yafi kyau, Hannah tawa.

100. **HANNAH:** Haka ne.

101: **KANDE:** Kun shawarta wace irin tazarar haihuwa za kuyi amfani da ita bayan kin haihu?

102: **HANNAH:** Hmm! Mama, bari in haihu mana tukuna, Kafin in fara tunanin wannan.

103. **KANDE**: Ah Haba ya ta, ai da zafi-zafi akan bugi karfe.

104. **HANNAH:** Toh mama, bayan na haihu zan rinka yin kebabben shayarwa na wani lokaci.

105. **KANDE:** Wannan akan yi shi na wata shida ne kawai ba tare da an baiwa jaririn wani abinci ko abin sha ba har sai kin fara haila. Ya kamata kiyi tunanin wani abu da zai dauki lokaci mai tsawo.

106. **HANNAH:** Kinyi gaskiya, Mama Ina amfani da kwayoyin magani ne da, amma ni da Danjuma mun shawarta Chanza wa zuwa wani wanda zai dauki lokaci mai tsawo.

107. **KANDE:** Ku duba duk hanyoyin da suke bayyane, sannan ku ajiye sakamakon har zuwa lokacin da za ku bukace shi, amma na jinjina muku da ku ka shawarta a tsakanin ku. Ni ina amfani da IUD ne.

108. **HANNAH:** Haka ne mama, Ina tunanin amfani da irin wannan ko kuma ashanar Fata.

109. **KANDE:** Toh ni dai na sami gogewa wurin amfani da IUD din, kuma hankalina ya kwanta dashi. Watakila kema zaiyi miki kyau.

110. **HANNAH:** Mmmm, Mama na gode.

111. **KANDE:** Ko da yake na san ba a bin da ya kawo Ki kenan ba Hannah.

112. **HANNAH:** Mama, na kanzo in ziyarceki ko wane lokaci.

Amma gaskiya ne, na kawo karar Tina ne. yau da safe na farka na ga tana wanke kamfen mijina.

113. **KANDE:** Haba! Ke Kika sa ta, Hannah?

114. **HANNAH:** Kalle ni mama bani na sata ba! Kwana biyu da suka wuce, na kamata tana kara kayan dandano a miyar da na yiwa mijina.

115. **KANDE:** Ah wannan bai dace ba, ko da yake watakila ba ta sani ba ne.

116. **HANNAH:** A zahiri bata sani ba. A gaskiya hankali na bai kwanta ba da zamanta a cikin gidan mu ba.

117. **KANDE:** Mmmm! Hannah!

118. **HANNAH:** Mama, Ko zata zo ta zauna da ke ne?

119. **KANDE:** Gaskiya bai kai ga haka ba, Hannah kiyi tunanin inda abin zai kasance. Yar uwarkice kuma mutane za suce kin kore ta daga gidanki.

120. **HANNAH: (INCENSED)** Kalli Mama, aure na yana da Mahimmanci a gareni. Har ma ta kai karana wurin maigidana, Ya Kirani yana lallashi na in yi hakuri da ita.

121. **KANDE:** Ki kwantar da hankalin ki Hannah, Kin san Yar uwarki ce. Bana kuma son wahalar yanuwa, zanyi mgana da ita.

122. **HANNAH:** Don Allah Mama, ya Kamata Kiyi Magana da ita.

123**. MUSIC: <u>BRIDGE UP AND FADE UP AND UNDER</u>**.